# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da



# Haifuwar Ikkilisiya


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**






**Bayan da Yesu mutu, matsorata masu binsa suka boye kansu. Bayan da Yesu ya tashi daga matattu, ya nuna kansa ga almajiransa. Yesu yana da rai! Amma – Yesu ya shirya zai bar su, don ya koma sama inda tun da ma yake kasancewa tare da Allah, Ubansa.**


Kafin ya bar su, Yesu ya yi wa masu binsa alkawari cewa zai aiko da Ruhun Allah don ya zama abin ta’aziya da Mai taimako. (Yohanna 15:26). Lokaci ya yi kusa! ‘Yan kwanaki bayan da Yesu ya tafi, Allah Ruhu Mai Tsarki ya zo.
3
Ga yadda ya faru. Masu bin Yesu waje 120 suna addu’a tare a wani gida. Nan da nan, gidan ya cika da amo na iska mai tsananin motsi.
4
Sai ‘yan kunshin wuta suna sauko a kan kowanensu. Dukansu aka cika su da Ruhu Mai Tsarki – daidai kamar yadda Yesu ya yi alkawari.
5
Sai suka fita a tituna, masu bin Yesu suka fara maganganu a harsunan ba su koya ba. Bakin da suke a Urushalima suka ji almajirai suna magana game da ayyukan ban mamaki na Allah a yaruruka dabam-dabam. Bakin suka yi mamaki. “Mene ne manufan wannan?” suna tambaya. “Sun koshi da sabon ruwan inabi ne,” wadansu suna musu gori.
6
Amma Bitrus ya ce, “Wadannan ba buge suke ba… wannan shi ne abin da annabi Yowel ya yi magana a kai…” Bitrus ya tunashe su abin shekarun baya, Allah ya yi alkarin Ruhu Mai Tsarki wanda zai zo ya alnarkace ya kuma taimake mutane.
7
Bitrus ya gaya wa mutanen dole sai sun tuba daga zunubansu a kuma yi musu baftisma a cikin sunan Yesu Kiristi… “kuma za ku karbi kyautan Ruhu Mai Tsarki,” Bitrus ya ce. Mutane wajen dubu uku 3000 suka yi biyayya. Suka hada kai da almajiran suka zama masu yin wa Yesu sujada. Yayinda lokaci na wucewa, mutane suka yi ta karuwa a cikin ikkilisiyar da Allah ya fara a ranar da Ruhu Mai Tsarki ya zo.
3000
8


Ruhu Mai Tsarki ya kawo ikonsa a cikin rayuwar mutanen Allah. Wata rana, Bitrus da Yohanna sun haura zuwa haikali tare asa'a na addu'a. Wani gurgu maroki yana zaune a waje bakin kofar haikalin. Ya roki kudi daga Bitrus da Yohanna.
9


Sai Bitrus ya ce, "Azurfa ko zinariya ba ni da shi, amma abin da nake da shi na ba ka: A cikin sunan Yesu Kiristi na Nazaret, tashi ka yi tafiya." Sai yadauke shi a hannun dama ya daga shi sama. Sai shi, cikin tsalle a tsaye, ya tashi ya kuma yi tafiya ya shiga cikin haikalin tare da su - yana tafiya, yana tsalle, yana yabon Allah.
10


Babban taron jama'a suka taru, suna mamkin al'ajibin. Bitrus ya gaya musu cewa ikon Allah ne ya yi haka, ba ikon kansa ba ne. Wanda ya warkar da gurgun. Sa'ad da Bitrus ya tunashe Yahudawan yadda Allah ya ta da Yesu daga mutuwa, shugabanan haikalin cikin fushi suka kama Bitrus da Yohanna suka saka su a kurkuku. Amma duk da hak, mutane waje 5000 suka ba da gaskiya a cikin Yesu.
11


Washegari, Bitrus da Yohanna suka tsaya a gaban shugabanan Haikalin. "Ta wurin ikon wane ne ko ta wurin sunan wane ne kuke yin wannan?" shugabanan suka tambaya. Cike da Ruhu Mai Tsarki, Bitrus cikin karfin hali ya amsa. "… ta sunan Yesu Kiristi na Nazaret, wanda kuka giciye, wanda Allah ta tashe shi daga matattu, ta wurin wannan ne wannan mutum yana tsaya a gabanku lafiya lau."
12


Bitrus ya ci gaba babu tsoro, "…babu wani suna a karkashin sama wanda aka ba wani mutum wanda za mu sami ceto." Don ba sa so mutanen sun ba da gaskiya ga Yesu, sai shugabanan suka ba Bitrus da Yohanna tsoro. "Daga yanzu har zuwa gaba, kada ku yi magana da wani game da sunan Yesu."
13


Bitrus ya taba jin tsoro ya tsare Yesu. Amma lokacin Ruhu Mai Tsarki ba zai zo ba tukuna.
Yanzu babu wanin da zai tsorotar da shi kuma. Bitrus da Yohanna suka amsa, "Ko daidai ne a gaban Allah mu saurare ku fiye da Allah, sai ku shari'anta. Gama mu kam ba za mu bar yin magana game da abubuwan da muka gani muka kuma ji ba."
14

Bayan barazanan da yawa daga shugabanan haikalin, sai suka sake Bitrus da Yohanna. Yan hidimar Allah masu karfin zuciya suka gaya wa abokan aikinsu game da kurkukun da kuna kotun. Sa'an nan suka yi babban taron addu'a da wakokin yabo. Kuma, Ruhu Mai Tsarki na Allah ya cika mutanen da iko – sai 'yar jaririn ikkilisiya ta yi girma.





**Haifuwar Ikkilisiya**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Ayyukan Manzani 1-4**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**






55 60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**